# Ka guji duniya sai Allah Ya so ka, ka guji abin da ke hannun mutane sai mutane su so ka

Daga Abul Abbas Sahlu ibnu Sa'ad al-Sa'idi - Allah Ya yarda dashi - ya ce: Wani mutum ya zo wurin Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi -, sai ya ce: Ya Manzon Allah, ka shiryar da ni akan aikin da idan na aikata shi Allah zai soni mutane ma za su so ni, sai ya ce: «Ka guji duniya sai Allah Ya so ka, ka guji abin da ke hannun mutane sai mutane su so ka».

[Nawawi ya ce: Hadisi ne mai kyau] [Ibnu Majah da waninsa ne suka ruwaito shi da isnadai kyakkyawa]

Wani mutum ya tambayi Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya shiryar da shi zuwa aikin da idan ya aikata shi Allah zai so shi kuma mutane ma zasu so shi, sai (Annabi) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce: Allah zai so ka idan ka bar mafifici a duniya, da abin da ba zai amfaneka a lahira ba, kuma ka bar abin da zai iya yi wuwa a cikinsa akwai cutarwa a Addinika, kuma mutane zasu so ka idan ka guji abinda ke hannunsu na duniya; domin su a ɗabi'arsu suna sonta, wanda kuwa ya yi gogayya da su a kanta zasuƙi shi, wanda ya bar musu ita zasu so shi.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee